# DUNIYAR FACEBOOK A YAU

*Jerin Takarda ta uku 003*

**Gabatarwa:** Basheer Journalist Sharfadi

(Shugaban Cibiyar Bincike Da Wayar Da Kan Al'umma Akan Amfani Da Shafukan Yanar Gizo-Gizo Ta **Sharfadi.com**)

No. 31 Sharfadi Quarter Kano, Nigeria.

Takarda A Babban Taron Kungiyar Wayar Da Kan Matasa Akan Siyasa Ba Da Gaba Ba Ta **DUNIYA MAI FADI** Wadda Aka Gabatar Ranar **Asabar 14 August 2018**, A Dakin Taro Na **Murtala Muhammad Library** Dake Kano.

## Contacts:

**Email:** info@sharfadi.com

**Facebook:** www.facebook.com/journalistsharfadi

**Twitter:** www.twitter.com/bjournalist55

**Instagram:** www.instagram.com/journalist55

**Call & WhatsApp:** +2349035830253

**Website:** www.sharfadi.com

#BasheerSharfadi #GaskiyaDaGaskiya #DuniyaMaiFadi

**Bangarori:**

i. Gabatarwa
ii. Ma'anar Social Media
iii. Meye Banbancin Social Media Da Sauran Kafafan Yada Labarai?
iv. Yadda Zaka Kare Account Dinka Na Facebook
v. Wasu Daga Abubuwan Da Yakamata Ka Lura Dasu A Facebook
vi. Me Yakamata Ka Rubuta A Facebook?
vii. Shin Ana Bautar Da Mutane A Facebook?
viii. Yadda Zaka Sauke Video Daga Facebook Da Youtube.
ix. Wadanne Shafuka Yakamata Ka Mallaka A Yanar Gizo-Gizo?
x. Wadanna Manhajoji (Applications) Ne Zasu Taimaka Maka Wajen Yin Ayyukanka A Social Media?
xi. Wadanne Kalubale Muke Fuskanta A Social Media?
xii. Wadanne Nasarori Muka Samu A Social Networks?
xiii. Shin Ta Yaya Masu Amfani Da Social Media Zasu Dinga Samun Kudin Shiga?
xiv. Rufewa.

## 1. Gabatarwa:

❖ Assalamu Alaikum warahmatullah, bayan sallama irin ta addinin musulunci, ina mai fatan alkhairi ga daukacin 'yan uwa da suka halarci wannan taro na wannan kungiya ta **Duniya Mai Fadi** kungiyar dake wayar da kan 'yan uwa matasa dangane da siyasa ba da gaba ba wadda **Talba Dan Abba Galadima** (Talban Dan Ruwatan Kano) yake jagoranta.

Wannan takarda zata zo a takaice sai dai dukkan batutuwan da zanyi magana akansu zaku iya samun cikakken bayani akai a www.sharfadi.com .

## 2. Ma'anar Social Media:

❖ Social Media Shafukane ko Manhajoji da zasu baiwa mutum damar tattaunawa da wani ta hanyar rubutaccen sako, hoto, hoto mai motsi (video) da kuma cikin sauti.

Mutane da dama kan tattauna batutuwa tare da musayar ra'ayi a wadannan shafuka.

Daga cikin wadannan shafuka akwai Facebook, Twitter, WhatsApp da sauransu.

3. **Meye Banbancin Social Media Da Sauran Kafafan Yada Labarai?**

❖ Akwai bam-bamci da dama tsakanin social media da kuma kafafan yada labarai na Radio da Talabijin, Misali yanzu idan muna da tashar Radio ko Talabijin a Kano, idan baka saurari shiri a wannan lokacin ba to shirin ya wuce ka, in banda yanzu da wasu tashoshin suke amfani da shafukan sadarwa wajen isar da sakonsu, su kuwa shafukan sadarwa ko baka gani a lokacin ba in ka hawo daga baya zaka gani.

Sannan idan iya gari ake suararon Radio to su Social Media sun hada al'umma daga dukkan yankuna wannan ya sanya sako anan yafi saurin tasiri fiye da na Radio.

Radio akan tan-tance labarai kafin a saki amman shi Social Media kana iya ganin tarin kanzon kurege.

4. **Yadda Zaka Kare Account Dinka Na Facebook:**

Yana da kyau mutum ya sanya ido matuka da gaske wajen lura da account dinsa na facebook duba da yadda satar account ta yawaita a facebook.

Zan fadi wasu daga muhimman abubuwa a takaice da yakamata ace mutum yayi don gudun fadawa wancan tarkon:

- ✓ Ka sanya Three Trusteed Contact (Mutane Uku Da Ka Aminta Dasu)
- ✓ Ka kara email address sama da guda daya account dinka, sannan kayi hiding dinsu.
- ✓ Ka cire duk wani apps da baka gasgata shi ba wanda kayi linking da facebook dinka.
- ✓ Ka cire lambar wayarka gaba daya daga facebook.
- ✓ Ka boye ranar haihuwarka daga facebook.
- ✓ Kada ka hade account dinka da wasu shafukan internet da baka tan-tance ba.
- ✓ Ka kaucewa yin login a facebook ta shafin da ba www.fb.com ko www.facebook.com ba.
- ✓ Ka sanya Password mai tsauri ba 123456 ko lambar wayarka ba.
- ✓ Ka ban-banta password din Email da kuma Facebook dinka.
- ✓ Ka guje baiwa wani email dinka wanda baka sani ba.

- ✓ Ka sanya login approval
- ✓ Ka dinga logout duk sand aka hau a waya ko computer wani.
- ✓ Ka daina yawan tura request.
- ✓ Ka daina sharing link din da baka tan-tance ba.
- ✓ Ka guji yin login a kowace browser (ina bada shawarar kayi amfani da google chrome).

## 5. Wasu Daga Abubuwan Da Yakamata Ka Lura Dasu A Facebook:

❖ Akwai abubuwa da dama da yakamata ka lura dasu a shafinka na facebook domin zasu taimaka maka wajen isar da sakon da kake son isarwa ga kadan daga ciki:

- ✓ Ka rufe Wall dinka daga tagging ya zama koda anyi tagging dinka ba za'a gani a wall dinka ba har sai ka duba sannan kayi approving.
- ✓ Ka mayar da privacy dinka na facebook ya koma "public".
- ✓ Ka sanya alamar "follow" a account dinka.
- ✓ Ka kaucewa shiga shafuka da groups na batsa na badala.
- ✓ Ka hade account dinka na facebook da twitter.

## 6. Me Yakamata Ka Rubuta A Facebook?

❖ Dan uwa yakamata kayi nazari kwarai da gaske kasan me zaka rubuta ko me zaka saka a facebook dinka?

- ✓ Ka kaucewa rubutukan cin zarafin wasu domin zasu iya maka ka a kotu su nemi hakkinsu.
- ✓ Ka kaucewa saka hotunan da suke nuna batanci ga wasu.
- ✓ Ka kaucewa saka hotunan tayar da tarzoma ko na fadan kabilanci ko na addini.
- ✓ Ka kaucewa saka hotunan hatsari ko rikici da zasu dagawa al'umma hankali.
- ✓ Kayi amfani da salon shagube ko gugar zana a duk sanda kake son isar da sako mai kama da wancan, kada ka kuskura ka kama sunan wani.
- ✓ Ka tabbatar da labari kafin ka yada.
- ✓ Ka dinga amfani da **Hash Tag** a rubutukanka.

## 7. Shin Ana Bautar Da Mutane A Facebook?

- Eh tabbas ana amfani da facebook wajen bautarwa musamman ga ‘yan uwa matasa ba tare da sun fuskanta ba, Misali ka zama baka da alkibla sai abinda wani yake so koda kuwa abin nan ya saba da maslaha ta al’umma ko kuma zai cutar da al’umma.

  Matasa Kashi Uku sukan fada cikin wannan hatsari:
  - ✓ **Kashi na farko:** Matasa da suka taso da kishi da zuciya ta gwagwarmaya amman kuruciya tana damunsu. Don haka sai wadannan mutanen suyi amfani da wannan kishin da yaran ke dashi su dinga kokarin juyasu ta hanyar sai abinda suke so zasu rubuta, duk sanda kuma Allah yasa idonsu ya bude suka balle to irin wadannan yaran mafi yawa zaka ga Allah ya sanya musu tasiri kuma akarshe suna zamowa barazana ga irin wadannan mutanen.
  - ✓ **Kashi na biyu:** Suna yin irin wannan rayuwarne domin neman yarda a wajen wadannan iyayen gidan nasu, da yawa zaku ga mutum da darajarsa amman ya koma dan jagaliya a facebook.
  - ✓ **Kashi na uku:** Su kuma su kan samu wani a facebook da yayi karfi sai su like masa komai yayi dai-dai ne ba don komai ba sai don suma su samu yawan comment in sunyi nasu posting din.

- **Su Waye Ke Bautar Da Matasa A facebook?**
  - ✓ ‘Yan Siyasa Sune Suka Fi Kowa Wajen Bautar Da Matasa Ta Hanyar Sanya Su Suyi Batanci Ga Abokanan Adawarsu, Wanda Sau Tari Idan Matashi Yana Tsananin Kaunarsa Ya Kan Iya Bayar Da Rayuwarsu Kacokan Wajen Kare Muradansu, Matasa Da Yawa Sukan Wayi Gari Cikin Wannan Kangin Bautar Ba Tare Da Sun Fuskanta Ba.
  - ✓ Masu Kudi Da Masu Neman Suna Suma Su Kan Bautar Da Mutasa Sosai Da Sosai A Kafar Facebook Ta Hanyar Tallan Muradansu.
  - ✓ Malaman Addini Wasu Daga Malaman Addini Kan Taka Muhimmiyar Rawa Wajen Bautar Da Matasa Ta Hanyar Sanya Su Cin Zarafin Malaman Da Suka Sabawa Wanda Wannan Yayi Tasiri Matuka Wajen Kara Haifar Da Gaba Tsakanin Musulman Nigeria, Sannan Mabiya Malam Wane Sukan Iya Cin Zarafin Duk Wanda Ya Sabawa Malaminsu Ta Kowace Hanya Misali Na Kusa Labarin **Dr. Sheriff Almuhajir** Yadda Akayi Amfani Da Wata Yarinya Domin Cin Zarafinsa Babu Sidi Ba Sadada.

8. **Yadda Zaka Sauke Video Daga Facebook Da Youtube.**

❖ Akwai hanyoyi da dama da ake sauke video amman za muyi bayanin hanya guda itace amfani da www.en.savefrom.net .

9. **Wadanne Shafuka Yakamata Ka Mallaka A Yanar Gizo-Gizo?**
    - ❖ Wadannan Shafukane Da Yakamata Ace Dan Gwagwarmaya A Wadannan Dandali Yakamata Ya mallakesu, musamman:
        - ✓ **Facebook:** Saboda shafine da yake da tasiri sosai kuma yake da sauri wajen tafka muhawara da musayar ra'ayi akwai Miliyoyin jama'a a wannan dandali, kuma bayan account yana da kyau mutum ya mallaki page a facebook.
        - ✓ **Twitter:** Shafine da yake da matukar tasiri sai dai har yanzu ana iya cewa mutanen mu anan Kano basu mayarda hankali akansa ba. (Idan ka bude twitter sai ka hadeshi da facebook dinka ya zama duk posting din da kayi zai tafi kan twitter dinka).
        - ✓ **Youtube:** Shafine da zai baka damar dora Videos akan sa.
        - ✓ **Kiwi6.com/Sound Cloud:** Shafukane da zasu baka damar sanya audio akansu.
        - ✓ **LinkedIn:** Shafine da zai baka dama ka dam aka sanya hakikanin ingantaccen tarihin rayuwarka.
        - ✓ **Website:** idan kana da website dukkan wadancan abubuwa zaka iya sanyawa akansa.

10. **Wadanna Manhajoji (Applications) Ne Zasu Taimaka Maka Wajen Yin Ayyukanka A Social Media?**
    - ❖ Applications ne da yakamata ace ka mallaka saboda irin taimakon da zasu yi maka wajen gudanar da ayyukanka, zamu yi magana akan apps na waya:
        - ✓ **Super Voice Recorder:** Zata taimaka maka wajen daukar sauti me kyau tatacce kuma a format na mp3.
        - ✓ **Adobe Audition:** Zata taimaka maka wajen gyara sauti.
        - ✓ **Viva Vedio:** Za Kayi amfani da ita wajen gyara Video.
        - ✓ **Inshot:** Za Kayi amfani da ita wajen gyara Video.
        - ✓ **Photo Editor:** Za Kayi amfani da ita wajen gyara hoto.

- ✓ **Videro Compressor:** Za kayi amfani da ita wajen rage nauyin Video.
- ✓ **Audio Compressor:** Za Kayi amfani da ita domin rage nauyin audio.

## 11. Wadanne Kalubale Muke Fuskanta A Social Media?

❖ Akwai tarin kalubale da masu amfani da shafukan sadarwa ke fuskanta daga ciki akwai.

- ✓ Shafukan karya
- ✓ Yaduwar Hotuna da Video na karya
- ✓ 'Yan Damfara
- ✓ Karin Yaduwar Munanan Akidu
- ✓ Yaduwar Fatawoyi Marasa Inganci
- ✓ Yaudara
- ✓ Yada Badala Iri-Iri
- ✓ Rura Wutar Rikici da Gaba tsakanin al'umma.
- ✓ Rashin iya tan-tance hakikanin labara
- ✓ Rashin Manufa a Shafukan
- ✓ Rashin Sirri Ta Yadda Kowa Zai Iya Sanin halin da kake ciki.

## 12. Wadanne Nasarori Muka Samu A Social Networks?

❖ Akwai tarin nasarori da shafukan sadarwa suka samar ga kadan daga cikinsu:

- ✓ Muna iya gudanar da taro a social media, ta yadda kowa yana gidansu zamu tattauna.
- ✓ Samun alaka da mutane ta kai tsaye
- ✓ Muna iya tallatawa jama'a wata haja tamu domin su siya
- ✓ An samu karuwar ilimi ta Social Media domin a yanzu har karatu ana iya yi ta nan.
- ✓ Samar da sana'a, Karin samun kudin shiga.
- ✓ Isar da sako cikin gaggawa.
- ✓ Samun sauki wajen mu'amala da hukumomi makarantu bankuna da sauransu.

## 13. Shin Ta Yaya Masu Amfani Da Social Media Zasu Dinga Samun Kudin Shiga?

❖ Akwai hanyoyi da dama da ake samun kudi a shafukan sadarwa na yanar gizo-gizo amman ga kadan daga ciki:

- ✓ **Karbar talla:** duk sanda kayi karfi a shafukan sadarwa zaka iya karbar tallan al'umma ka tallata musu domin samun abokanan ka suwanci kai kuma su biyaka.
- ✓ **Amfani da Tunaninka:** Zaka iya kirkiro wani abu da mutane ke da bukatarsa shima zai dinga kawo maka kudin shiga.
- ✓ **Adfly:** Shafi ne da zaka sanya musu link dinka ta yadda idan mutum ya shiga wannan link din naka ba zai yiwu ya kaishi ga asalin sakon ba har sai yaga tallansu, su kuma da wannan tallan zasu dinga biyanka.
- ✓ **Youtube:** idan kana da Youtube Channel kana sanya Videos, za kayi register **Google Adsense** wanda in ka samu **Subcribers 1,000 Viewers 10,000** kana da **$100 .**
- ✓ **Website:** Idan kana da Website shima zaka yi register da **Google Adsense** zasu dinga sanya maka talla akan website dinka ta yadda duk sanda wani ya shiga zai ga talluka akai, idan mutane 10,000 suka danna tallan nan shima kana da **$100.**

**14. Rufewa:**

- ❖ Kamar yadda nayi bayani tun a farko zaku iya samun cikakkun wadannan bayanan a babban shafi na www.sharfadi.com.
  Ina fatan wannan bayani nawa yayi amfani gareku 'yan uwa matasa, sannan kofa a bude take ga duk sanda kuke da wasu shawarwari ko Karin haske ina maraba da ku, Assalamu Alaikum.

## Jerin Takardun Da Suka Gabata:

1. **Takardar SaniN Makama**

**Ga Daliban Da Zasu Zana Jarabawar Jamb**

2. **Mu Koyi Computer A Saukake**

***Zaku Iya Samun Wadannan***

***Takardu a* www.sharfadi.com**

## Contacts:

**Email:** info@sharfadi.com

**Facebook:** www.facebook.com/journalistsharfadi

**Twitter:** www.twitter.com/bjournalist55

**Instagram:** www.instagram.com/journalist55

**Call & WhatsApp:** +2349035830253

**Website:** www.sharfadi.com